

ARDP

# Rahoton 2021

## Akan Ayyukan Raya MazaɓunTarayya Na Jihar Zamfara

*Da Tallafin:* MacArthur Foundation

# GABATARWA

Bibiyar ayyukan mazaɓu a jihar Zamfara na ɗaya daga cikin ayyukan ƙungiyar Nazari da Ƙoƙarin Ciyar da Arewa Gaba (ARDP); a matsayin ɗaya daga cikin shirye-shiryen da gidauniyar MacArthur ke tallafamawa a ƙarƙashin shiri mai take da "On Nigeria 2.0". Manufofin shirin sun mayar da hankali ne kan rage cin hanci da rashawa ta hanyar taimaka wa shirye-shirye da yunƙurin al'umma da za su ƙarfafa al'adar riƙon amana, gaskiya da kuma sa hannun jama'a wajen gudanar da al'amuransu. Ɗaya daga cikin manyan maƙasudin wannan aiki shi ne tantance matakan shigar da al'ummomi daban-daban wajen ƙirƙirowa da aiwatar da ayyukan mazaɓu da nasabarsu da bukatun al'umma. Har ila yau, ana sa ran aikin zai samar da tsari ko kuma ƙara sa ƙaimi ga 'yan kasa wajen ƙirkiro da ayyukan mazaɓu da kuma zaburar da al'umma wajen sa ido da bin diddiƙin ayyukan. Wannan aikin ƙungiyar ZamTracka ce, abokiyar hadin gwiwa a jihar Zamfara, ke aiwatarwa.

Ƙungiyar ARDP dai wata cibiya ce mai bincike da bata da alaƙa da gwamnati ko la'akari da wata siyasa, ƙabila, ko nuna bambancin addini wadda ayyukanta sun mayar da hankali wajen nazari da tantance manyan matsaloli da ke addabar Arewacin Nijeriya da al'ummarta, da yunƙurin samar da hanyoyin bincike da tsare-tsaren ayyukan da zasu magance matsalolin dake addabar yankin. Gurin Cibiyar shine ƙoƙarin samar da tafarkin bunƙasar tattalin arziki da kyautata rayuwar al'ummar yankin ta hanyoyin da zasu samar da haɗin guiwa tsakanin jama'a da hukomomin gwamnati wajen hada ƙarfi-da-ƙarfe  domin ciyar da al'umma gaba..

Ita kuwa ZamTracka, ƙungiya ce mai zaman kan ta da ke Gusau a jihar Zamfar, wadda ta ke yekuwar ganin ana yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a a cikin mulkin jihar. Fitattun ayyukan ta sune samowa da tantance bayanai kan tanade-tanaden ayyuka da ke cikin kasafin kuɗi na jihar Zamfara da kuma ayyukan raya-ƙasa a yankunan mazaɓu, da kuma yin amfani da su wajen wayar da kan al'umma. Manufa dai ita ce a taimaka wa jama'a wajen bin diddiƙin tanade-tanade kasafin kuɗi da yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu. Ana san cewa wannan yunƙuri zai sa

a samu masu himma da dagewa wajen ganin ana gudanar da ayyukan raya-ƙasa na gwamnati da hukumominta tare da haɗaka yadda jama'a za su nemi samun ]orarriyar hanyar tsoma bakinsu a cikin gudanar da al'amuran jiharsu.

Ayyuka na shiyya, wanda aka fi sani da ayyukan mazaɓu, ayyuka ne na jama'a da 'yan majalisar tarayya sukan gabatar domin kawo ribar mulkin demokaraɗiyya ga al'ummominsu don haɓakar ci-gaban yankunan karkara. A kan gabatar da bukatun gudanar da waɗannan ayyukan ne ga sashen mulki a lokacin da ake tsare-tsaren kasafin kuɗi. Tsarin mulkin ƙasa ya tanadi cewa majalisun tarayya ke da alhakin sanya ido akan ayyukan gwamnati. Kasancewar 'yan majalisu ne ke ƙirƙirar ayyukan, ashe su ke da nauyin su riƙa yiwa jama'a bayanai akai-akai akan ayyukan. Wannan ya isa hujja saboda talakawa ba za su iya tunkarar hukumomin gwamnati cikin sauƙi ba kamar yadda za su iya tuntuɓar wakilan su. Domin ganin munbi diddiƙin waɗannan ayyukan raya ƙasa akan kari, mun yi amfani da jami'an mu waɗanda suka san wuraren da ake gudanar da takamaiman ayyukan.

A shekarar 2022, an ware jimillar Naira Biliyan 2.24 don gudanar da ayyukan mazaɓu a Zamfara, mafi yawansu ayyukan horarwa da talaffi ne. Manyan ayyuka sun haɗa da samar da abubuwan more rayuwa na zahiri, kamar gina hanyoyi ko makarantu, yayin da ayyukan horarwa da tallafi suka fi mayar da hankali kan haɓaka ƙwarewa da iya aiki a cikin al'umma. A jihar Zamfara, manyan ayyuka na iya bada gudummawa ga inganta tsarin ababen more rayuwa, yayin da ayyukan horarwa da tallafi ke nufin ƙarfafa mutane da haɓaka ci gaba mai dorewa ta hanyar gina fasaha da ilimin su. Dukansu suna taka muhimmiyar rawa a cikin ci gaban al'umma, ta hanyar magance fannoni daban-daban na ginuwar al'umma. Sai dai babban abin da ke faruwa a jihar Zamfara shi ne, ayyukan horarwa da tallafi ba'a ƙiƙirosu da gudanar da su ta hanyar da za a cimma alfanunsu.




# MAZABAR GUSAU/TSAFE

**3** Yawan Ayyuka

**3** Aka Aiwatar

**0** Ba ayi ba

# Taimakawa Mata da Matasa a Mazaɓar Tarayya ta Gusau/Tsafe

**N40m**

**An Aiwatar**

Tun da farko an tsara aiwatar da wannan aikin na tsawon kwanaki hudu (4) ne, daga ranar 12 zuwa 16 ga Oktoba, 2021 amma an gudanar da shirin ne kawai a ranar 12 ga Oktoba 2021. Mutane 600 waɗanda suka fito daga gundumomi 11 na ƙaramar hukumar Gusau ne aka kasafta zasu amfana daga wannan shirin da aka ƙaddamar a cibiyar horaswa ta UBE, Gusau. Amma mutane kamar 200 ne kawai suka sami horon. An karantar da waɗanda suka ci gajiyar shirin kan dabarun kasuwanci da yadda ake farawa da sarrafa ƙananan sana'o'in kasuwanci.

A ƙarshen zaman laccar, kowane ɗaya daga cikin waɗanda suka amfana ya karɓi kuɗi Naira 25,000 a matsayin jarin farawa. Ba a sani ba ko akwai wani shiri na tantancewa da sa ido domin tabbatar da ci gaba da la'akari da ƙalubalen da aka samu wajen aiwatar da wannan shirin.








# Taimakawa Mata da Matasa a Mazaɓar Tarayya ta Gusau/Tsafe

**N40m**

**An Aiwatar**

Tun da farko an tsara aiwatar da wannan aikin na tsawon kwanaki uku (3) ne, daga ranar 16 zuwa 18 ga Oktoba, 2021 amma an gudanar da shirin ne kawai a rana guda. Mutane 600 waɗanda suka fito daga gundumomi 11 na ƙaramar hukumar Tsafe ne aka kasafta zasu amfana daga wannan shirin da aka ƙaddamar a cibiyar horaswa ta UBE, Gusau. Amma mutane kamar 200 ne kawai suka sami horo kan dabarun kasuwanci da yadda ake farawa da sarrafa ƙananan sana'o'in kasuwanci.

A karshen zaman laccar, kowane daya daga cikin wadanda suka amfana ya karbi kudi naira 25,000 a matsayin jarin farawa. Ba a sani ba ko akwai wani shiri na tantancewa da sa ido domin tabbatar da ci gaba da la'akari da ƙalubalen da aka samu wajen aiwatar da wannan shirin.








# Taimakawa Mata da Matasa a Mazaɓar Tarayya ta Gusau/Tsafe

**N40m**

**An Aiwatar**

An gudanar da wannan aikin ne daga ranar 11 zuwa 13 ga watan Nuwambar 2021. Wannan shirin haɗin gwiwa ne inda aka shirya jimillar masu cin gajiyar shi 2,000 zasu fito daga dukan gundumomi 22 na mazaɓar kuma 1,400 daga cikinsu mata ne. Shiri ne na horaswa a kan sana'o'in hannu a kan ɗinki da yin kayan kwalliya da aka gudanar a cibiyar horaswa ta UBE da ke Gusau. Ko da yake an karkasa tsarin aiwatar da shirin, kaɗan ne kawai na adadin waɗanda aka yi niyya suka sami horon.

A ƙarshen zaman laccar, kowane ɗaya daga cikin waɗanda suka amfana ya karɓi kuɗi Naira 25,000 a matsayin jarin farawa. Ba a sani ba ko akwai wani shiri na tantancewa da sa ido domin tabbatar da ci gaba tare da la'akari da ƙalubalen da aka samu wajen aiwatar da wannan shirin.










Hon. Shehu Ahmad

# MAZABAR BUNGUDU/MARU

**3** Yawan Ayyuka

**2** Aka Aiwatar

**1** Ba ayi ba

# Horo da Karfafawa Mata da Matasa a Mazaɓar Tarayya ta Bungudu/Maru

**N40m**

**An Aiwatar**

An gudanar da wannan aikin ne a ranar 19 ga watan Oktoba, 2021 a dakin taro na otal din Fulbe Villa dake yankin Mareri, a ƙaramar hukumar Gusau. Mutane 250 ne daga gundumomi ashirin da ɗaya (21) na mazaɓar aka lissafa zasu amfana daga shirin. An yi wa waɗanda suka ci gajiyar lacca kan yadda ake amfani da injuna wajen aikin dogaro da kai.

A ƙarshen zaman horon, mazaje da suka ci gajiyar tallafin sun samu kekunan ɗinki yayin da takwarorinsu mata suka samu injunan niƙa. Ba a sani ba ko akwai wani shiri na tantancewa da sa ido domin tabbatar da ci gaba tare da la'akari da kalubalen da aka samu wajen aiwatar da wannan shirin.








# Horo da Karfafawa Mata da Matasa a Mazaɓar Tarayya Bungudu/Maru

**N40m**

**An Aiwatar**

Wannan shirin tallafi ne na aikin gona. An zaɓo mutane uku (3) a kowace gunduma cikin gundumomi ashirin da ɗaya (21) na mazaɓar domin cin gajiyar wannan shirin kuma an karantar da su kan dabarun noma don inganta ayyukan noma da haɓaka yawan amfanin gona.

An gudanar da horon na tsawon kwanaki biyu inda a ƙarshe kowanne ya samu buhunan taki da injin feshi da kuma sinadarai masu alaƙa da aikin gona. An gudanar da taron ne a dakin taro na otal din Fulbe da ke unguwar Mareri a ƙaramar hukumar Gusau.








# Samar da Injunan Nika da Dinki a Mazaɓar Tarayya ta Bungudu/Maru

N41m

Ba ayi ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.



Hon. Umar Dangaladima

# MAZABAR KAUR/BIRNIN MAGAJI

**3** Yawan Ayyuka

**2** Aka Aiwatar

**1** Ba ayi ba

# Shirin Bada Maganin Ciwon Idanuwa Kyauta ga Mata da Tsofaffi a Mazaɓar Tarayya ta Kaura Namoda / Birnin Magaji

**N30m**

**An Aiwatar**

Ainihin wannan aikin na taimakon kiwon lafiya ne kuma an ƙaddamar da shi ne a ranar 19 ga Nuwamba, 2021 a manyan asibitocin Kaura Namoda da Birnin Magaji. An yi niyya ne musamman ga tsofaffi masu nau'ikan matsalolin ciwon ido waɗanda ke da sauƙin magancewa. Adadin tsofaffi 510 ne suka amfana daga wannan shirin. Kimanin 200 daga cikinsu an ba su tabarau yayin da sauran waɗanda suka ci gajiyar shirin aka basu magunguna don cututtukan ido daban-daban.

Mutanen da suka bayyana tare da ciwarwatan ido mai ƙarfi an basu shawarar da su tafi cibiyoyin kiwon lafiyar ido don neman magani. Dangane da tasirin shirin kuwa, wannan taimakon ya sami yabo sosai domin waɗanda suka karɓi magani ba su da wata hanyar neman magani a ƙashin kansu, don haka wannan taimakon bada gudumuwar wajen inganta rayuwar waɗanda suka ci gajiyar shirin. Ba mu sani ba ko akwai wani tsari na bin sayun wannan shirin ko a'a.








# Samar da Mota Kirar Toyota Hilux Mai Daukar Mutum 18 a Mazaɓar Tarayya ta Kaura Namoda/Birnin Magaji

N24m

Ba ayi ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

# Horo da Karfafawa Matasa da Mata a Mazabar Tarayya ta Kaura Namoda/Birnin Magaji

**N40m**

**An Aiwatar**

Wannan shima shiri ne na ba da agajin noma wanda aka aiwatar a ranar 18 ga Maris, 2021. Waɗanda suka amfana galibi manoma ne daga kungiyoyin haɗin gwiwa da aka zaɓo daga dukkan gundumomin da ke mazabar. An ba wa waɗanda suka ci gajiyar shirin tallafi na ƙananan injunan noma. An ƙaddamar da shirin ne a ofishin jam'iyyar PDP na Kaura Namoda, cikin ƙaramar hukumar Kaura Namoda.

Maƙasudin tallafi dai akan ƙananan manoma ne domin su sami damar haɓaka samar da amfanin noman su zuwa ga samun rarar amfanin gona. Amma ba mu da bayani akan ƙa'idojin da aka yi amfani da su wajen zaɓar waɗanda suka amfana ba. Akwai yuwuwar aiwatar da irin waɗannan ayyukan ba tare da cikakken tsari ba na kawo cikas waje cimma manufofinsu.







Hon. Ahmad Muhammad

# MAZABAR BAKURA/MARADUN

**3** Yawan Ayyuka

**3** Aka Aiwatar

**0** Ba ayi ba

# Horo da Karfafawa Kungiyoyin Hadin Gwiwa a Mazaɓar Tarayya ta Bakura/Maradun

**N40m**

**An aiwatar**

Wannan wani shiri ne na aikin noma musamman ga ƙungiyoyin haɗin gwiwar na mazaɓar da ke aikin noman rani. Mutane 200 zuwa 300 a ke niyyar su ci gajiyar shirin. An bada horon ne na lacca ga waɗanda suka ci gajiyar shirin a Kwalejin Aikin Gona da ke Bakura, amma babu wasu darussa na nuna makakar aikin noma. Bayan zaman lacca, an bai wa kowannen su injin ban ruwa mai amfani da iskar gas a matsayin tallafi don bunƙasa amfanin aikin noma.

Ana ganin wannan shirin a matsayin tallafawa manoma a cikin al'ummar mazaɓar da sun dogara ne akan noma a matsayin jigon rayuwarsu. Sai dai babu wani tsari da ya dace a cikin dabarun aiwatar da shi don tantance irin tasirin da wannan aikin zai yi kan muhimman ƙalubalen da al'ummar mazaɓar ke fuskanta.







# Samar da Injunan Dinki da Babura a Mazaɓar Tarayya ta Bakura/Maradun

**N50m**

**An aiwatar**

Wannan aikin ba da taimako ne, wanda aka aiwatar a ranar 2 ga Yuli, 2021. An sayo injunan ɗinki da babura domin rabawa ga waɗanda aka zaɓo daga gundumomin mazaɓar. Ba a san ƙa'idojin zaɓar waɗanda suka ci gajiyar ba. Sai dai an gano cewa an raba injunan ɗinkin ne ga Mata yayin da aka raba baburan ga Maza.

An ƙara fahimtar cewa galibin waɗanda suka amfana da baburan makusantan dan majalisar ne a siyasance, wadanda akasarinsu ake kiransu ‘yan jarida'. Ba a iya tantance ainihin adadin waɗanda suka ci gajiyar wannan shirin ba domin tabbatar da gaskiyar ko an kashe yawan kuɗin da aka ware wa shirin.








# Gyaran Makarantun Firamare da Sakandire da Samar da Tebura da Kujeru a Mazaɓar Tarayya ta Bakura/ Maradun

N50m

An Aiwatar

Wannan aikin ya ƙunshi gina sabon katafaren gini mai ajujuwa guda shida (6) tare da gyaran wasu gine-ginen azuzuwa guda biyu (2) da sa kujeru, tebura da farin allon rubutu a cikin azuwawan a makarantar sakandiren 'yan mata ta Bakura. An fara aikin ne a kashi na biyu na shekara kuma an kammala shi a ranar 5 ga Disamba, 2021. Baya ga gina ƙarin ajujuwa na makarantar an katange ta a matsayin wani bangare na aikin. Haka kuma anyi amfani da den wannan aiki domin gyarawa da kuma samar da kayan aiki ga wasu makarantun islamiyya a mazaɓar.

A matsayin shirin tallafi ma ilimi, wannan aikin na da tasiri sosai kan bunƙasa ilimi a mazaɓar. Aikin ya taimaka wajen rage cunkoson ajujuwa a makarantar sakandiren 'yan mata ta Bakura tare da bayar da gudunmawa sosai ga harkar karatu a makarantun islamiyya da abin ya shafa.









Hon. Sulaiman Gummi

# MAZABAR GUMMI/BUKKUYUM

**3** Yawan Ayyuka

**3** Aka Aiwatar

**0** Ba ayi ba

# Horo da Karfafawa Mata na Kiwon Akuya a Mazaɓar Tarayya ta Gummi/Bukkuyum

**N40m**

**An Aiwatar**

Wannan shirin bada tallafi ne na karfafawa matan karkara. An aiwatar da shine a ranar 18 ga Nuwamba, 2021. An horar da waɗanda suka ci gajiyar shirin da aka zaɓo daga gundumomi 21 na mazaɓar kan dabarun kiwon akuya. Ba a san ƙa'idojin da aka bi ba wajen zaɓen ba da kuma ainihin adadin waɗanda suka amfana ba. An yi iƙirarin cewa an raba kimanin awaki 500 ga waɗanda suka ci gajiyar horon da suka haɗa da waɗanda ba su iya halartar horon ba amma an ba su akuya a matsayin tallafi a gidajensu. Da yawa daga cikin mazauna mazaɓar sun koka da yadda tsarin rabon bai bayar da shawarar samar da akalla akuyoyi guda biyu ba domin samun alfanun hayayyafa, wanda shine maƙasudin shirin.








# Samar da Kayan Koyarwa a Mazaɓar Tarayya ta Gummi/Bukkuyum

**N41m**

**An aiwatar**

Wannan wani shiri ne na tallafi na ilimi wanda ya shafi makarantun firamare da sakandare na gwamnati a mazabar. An aiwatar da aikin ne a ranar 8 ga Fabrairu 2022. Kayayyakin tallafin ilimi da aka saya don rabawa ga makarantun da aka yi niyya sune katin 50 na kwalin kayan lissafi; fakiti 163 na alkalami na rubutu; fakiti 500 na dasta to goge allon rubutu; na'urar daidata murabba'ai guda 150; allon rubutu guda150, fakiti 200 na rezar feƙe fensir; kwalaye 150 na farin alli; litattafan rubutu masu shafi 40 guda 3,156; lilitattafan rubutu masu shafi 60 guda 3,156; litattafan rubutu masu shafi 80 guda 3,156.

Sai dai ba a san takamaiman adadin makarantun da suka ci gajiyar wannan aiki da yadda rabon kayan yake ba.







# Horaswa da Karfafawa Mata da Matasa kan Magance Rikice-Rikice da Samun Zaman Lafiya a Mazaɓar Tarayya ta Gummi/Bukkuyum

**N40m**

**An aiwatar**

Wannan aiki dai yayi kama da aikin da dan majalisar ya gabatar a shekarar 2020. Aikin ya shafi manoman noman rani a karamar hukumar Bukkuyum wadanda aka horar da su kan dabarun noman noma kuma kowanne daga cikin wadanda suka ci gajiyar aikin ya samu na'urar samar da wutar lantarki. An raba wa matan kayayyakin fara kasuwanci na kananan sana'o'i da suka hada da injin dinki da injin nika. A cewar dan majalisar, an dauki matakin ne domin baiwa wadanda suka amfana damar dogaro da kai.

Kamar sauran irin wadannan ayyukan shiga tsakani a jihar, babu wani sharudda na zabar wadanda za su amfana da kuma rashin tsarin tantance irin wadannan ayyukan karfafawa da nufin tabbatar da tasirinsu da kalubalen da suke fuskanta ta yadda za a jagoranci wuraren da za a inganta a tsarin aiwatarwa od. irin wadannan ayyuka a nan gaba.











# MAZABAR ANKA/MAFARA

**2** Yawan Ayyuka

**1** Aka Aiwatar

**1** Ba ayi ba

# Samarda Kayan Aiki da Magunguna Don Kula da Mata da Yara a Cibiyoyin Kula da Maras lafiya a Mazabar Anka/Mafara

N100m

Executed

An gudanar da wannan shirin ne a ranar 24 ga watan Satumba 2021. An sawo kayan aikin jinya da suka haɗa da gadaje, katifu, durowoyin gadaje, kayan aikin tiyata da wasu kayan magunguna, an kuma ba da gudummawar su ga Babbar Asibitin Anka. Duk da cewa ba mu da cikakkun bayanai kan yawan kayan da kuma kuɗin na kayayyakin da aka bayar, jama'a da dama a mazaɓar sun yaba da tallafin bisa la'akari da halin da ake ciki a asibitin. Wannan tallafin ya taimaka wajen samar da ƙarin wurin kwanciya ga ƙarin majiyyata a cikin ɗakunan maras sa lafiya na asibitin. Hakazalika, sabbin kayayyaki na magunguna sun bada damar kula da ƙarin masu jinya a cikin ɗan gajeren lokaci.







# Gina Rijiyoyin Burtsatse a Mazabar Anka/Mafara

N21m

Ba Ayi Ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.



Hon. Bello Hassan Shinkafi

# MAZABAR SHINKAFI/ZURMI

**4** Yawan Ayyuka

**3** Aka Aiwatar

**1** Ba ayi ba

# Samar da Nabura da Injin Fanfo a Mazaɓar Tarayya ta Shinkafi/Zurmi

N50m

An Aiwatar?

An gabatar da wannan aikin ne a shekarar 2021 amma an aiwatar da shi a ranar 27 ga watan Agusta 2022. An ƙaddamar da shi a harabar ofishin jam'iyyar PDP na ƙaramar hukumar Shinkafi. A yayin bikin ƙaddamar da shirin an sawo babura goma (10) kuma an raba babura 6 ga waɗanda suka fito daga ƙaramar hukumar Shinkafi yayin da aka raba babura 4 ga wadanda suka fito daga ƙaramar hukumar Zurmi. Saɓanin taken shirin, babu injinan fanfo da aka rarraba a lokacin bikin ko bayan haka.

A ƙashin gaskiya, baburan 10 ɗin an raba su ne kawai ga na hannun damar ɗan majilisar da ya ƙirƙiro aikin, mutanen da ake ma laƙabi da 'yan jarida' na ɗan majalisar. Don haka ba abin mamaki ba ne cewa wannan aikin ba shi da kima ko tsarin da za a kira shi a matsayin wani aiki don amfanin jama'a. Bugu da ƙari, ko da a kan ma'aunin da aka ƙaddamar dashi ana iya cewa aikin bai kammala ba.







# Samar da Keke Napep a Mazaɓar Tarayya ta Shinkafi/Zurmi

N35m

An Aiwatar

An ƙaddamar da wannan shirin rana ɗaya tare da aikin da ya gabata inda aka raba babura 10. An kuma ƙaddamar d shi a daidai wurin da aka ƙaddamar da na baya; wato a harabar ofishin PDP dake ƙaramar hukumar Shinkafi.

A wannan shirin an raba keke napep ga shuwagabannin jam'iyyar ta PDP na unguwani a ƙananan hukumomi biyu da suka ƙunshi mazaɓar ta tarayya. Wannan aikin garaɓasa ce ga ƴan siyasa na mazaɓar saboda haka da ƙyar ya iya wucewa a matsayin aikin mazaɓa.







# Samar da injunan Nika da Dinki don Karfafama Mata a mazabar Tarayya ta Shinkafi/Zurmi

N36m

Ba Ayi Ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.



Sen. Lawali Hassan

# MAZABAR ZAMFARA TA YAMMA

**2** Yawan Ayyuka

**1** Aka Aiwatar

**1** Ba ayi ba

# Tallafin ga Matasa da Mata a Fadin Kananan Hukumomin Shiyyar Zamfara ta Yamma

**N214m**

**An Aiwatar**

An aiwatar da wannan aikin ne a ranar 14 ga Disamba, 2021 a Talata Mafara, ƙaramar hukumar Talata Mafara. Shiyyar Sanatan ta ƙunshi kananan hukumomi 6, don haka ne an zabo waɗanda ba a tantance adadin su ba daga dukkan ƙananan hukumomi guda 6 don amfana da shirin. Saboda rashin takamaiman ƙa'ida wajen zaɓen ne ya tabbatar da korafe-korafen cewa waɗanda aka zaɓa kusan dukkanin su 'yan siyasa ne masu biyayya ga dan majalisar. Dangane shirin kuwa, duk ya dogara ne akan lacca da wani ƙwararre ya gabatar kan sana'ar fina-finai. Shekaru da dama, 'yan majalisa daga wannan yanki na Jihar suna ƙirƙiro ayyukan da suka shafi harkar fina-finai; al'amarin da ba'a san jihar da shi ba.

A karshen taron, an baiwa kowane wanda ya ci gajiyar tallafin Naira 10,000 maimakon N20,000 da ke tsare cikin shirin aiwatar da aikin.








# Gina Rijiyoyin Burtsatse na Hannu a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Yamma

**N50m**

**Ba Ayi Ba**

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.











# MAZABAR ZAMFARA TA AREWA

**12** Yawan Ayyuka

**6** Aka Aiwatar

**2** An fara an bari

**4** Ba ayi ba

# Kamalla Hanyar Nasarawar Godel Zuwa Sabon Birni da Cigama Cikin Shiyyar Sanatan Zamfara ta Arewa

N150m

An aiwatar

Wannan titin karkara ne mai nisan kilomita 35, wanda ya haɗa kauyukan Nasarawar Godel da Cigama a ƙaramar hukumar Kaura. A yayin da ake bibiyar aikin da kuma sa ido bisa aikin, masu tantance ayyukan sun gano cewa duk da cewa wuraren akwai laka da zaizayar ƙasa ba a samar da magudanar ruwa ba, kuma ingancin aikin da akayi a ƙasa bai yi kyau ba. Bugu da kari, titin bai yi tsari ba saboda kwalta da tsakuwa kawai aka shimfiɗa. Wannan yana nufin cewa hanyar ba za ta yi ƙarko ba saboda yanayin ƙasar. Don haka, duk da tasirin da aikin zai iya yi ga al'umma, ba a aiwatar da shi ta yadda zaiyi cikakken tasiri ga harkokin more rayuwa da tattalin arzikin al'ummar yankin ba.







# Kamalla Hanyar Store Zuwa Mayasa Cikin Shiyyar Sanatan Zamfara ta Arewa

**N150m**

**An Bar Aikin**

Wannan hanyar karkara ce da aka fara a shekarar 2021 domin haɗa garuruwan Store da Mayasa a ƙaramar hukumar Zurmi. A lokacin da ake bibiyar wannan aikin, masu tantance ayyuka sun lura cewa an yi watsi da wannan aikin. A bayyane yake cewa an yi aikin share fage na tono da kuma gina ƙananan gadoji, kuma surar hanyar ya fito. A ci gaba da bincike kan dalilin da ya sa aka yi watsi da aikin, an sanar da masu tantance ayyuka cewa an yi garkuwa da wasu daga cikin ma'aikatan da ke aikin, inda nan take dan kwangilar ya kwashe ma'aikata daga wurin.

Duk nasarorin da aka samu a lokacin ayyukan share fage a yanzu sun lalace saboda hanyar a yanzu ta cika da zaizayar kasa sannan kuma ta gefen hanyar ya lalace saboda rashin magudanar ruwa.







# Kammala Hanyar Shinkafi Zuwa Shanawa Cikin Shiyyar Sanatan Arewacin Zamfara

N150m

An Aiwatar

Wannan titin karkara ne da aka fara a shekarar 2021 don haɗa garin Shanawa zuwa garin Shinkafi a cikin ƙaramar hukumar Shinkafi. A yayin da ake bibiyar aikin, masu tantance ayyuka sun lura da ingancin aiki kuma sun gano cewa an aiwatar da wannan aikin cikin gamsuwa. Aikin hanyar ya kasance mai inganci kuma an samar da magudanar ruwa. Ba kamar aikin hanyar Nasarawa Godel zuwa Cigama ba, an zuba ma titin kwalta mai kauri.

Wannan muhimmin titin karkara ne da ya haɗa hedkwatar ƙaramar hukumar Shinkafi da wani muhimmin gari na Shanawa, wanda yanki ne mai albarkar noma. Don haka, wannan aikin zai yi tasiri mai kyau a kan tattalin arzikin al'ummar yankin.







# Kammala Hanyar Sabon Gari Zuwa Kungurki da Daba Cikin Shiyyar Sanatan Arewacin Zamfara

**N200m**

**An Bar Aikin**

Wannan hanya ce ta karkara da aka fara a shekarar 2021 domin haɗa ƙauyukan Kungurki da Daba zuwa unguwar Sabon Gani a ƙaramar hukumar Kaura Namoda. A yayin da ake bibiyar aikin, masu tantance ayyuka sun gano cewa an yi watsi da wannan aikin titin na Kaura Namoda. A bayyane yake cewa an yi aikin share fage na farko, kuma an gina ƙananan gadoji da suka haɗa hanyar.

A ci gaba da bincike kan dalilin da ya sa aka yi watsi da shi, an gano cewa an bayar da wannan aikin ne ga dan kwangilar da ke aikin titin Store zuwa Mayasa da ke karamar hukumar Zurmi inda aka yi garkuwa da wasu daga cikin ma'aikatan da ke aikin, dalilin da ya sa dan kwangilar ya yi watsi da aikin nan take. Duk nasarorin da aka samu a yanzu sun lalace saboda hanyar a yanzu tana cike da zaizayar kasa sannan kuma ta gefe ta lalace saboda karancin magudanan ruwa.








# Sayen Kayan Rijiyoyin da Famfuna ga Kananan Hukumomin Kaura Namoda da Zurmi a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Arewa.

N50m

An Aiwatar

An gudanar da wannan aikin ne a ranar 16 ga Oktoba, 2021. Wannan tallafin aikin noma ne wanda akasari ya shafi manoman rani ne. An zaɓo waɗanda suka ci gajiyar shirin daga kowace gunduma a ƙananan hukumomi biyu kuma an ba su injin ban ruwa na aikin noman rani. Taron ƙaddamar da shirin ya gudana ne a harabar ofishin jam'iyyar PDP na Kaura Namoda.

Ba a iya tantance adadin waɗanda suka amfana ba. Har ila yau, ba a san ƙa'idojin da aka bi wajen zaɓen waɗanda suka ci gajiyar shirin ba. Kamar dai duk ayyukan bada horo da tallafi a cikin Jiha, waɗanda suka ci gajiyar wannan shirin galibin su abokan siyasa ne na ɗan majalisar.








# Samar da Magunguna da Kayayyakin Asibiti ga Asibitoci da Cibiyoyin Kula da Maras Lafiya a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Arewa.

N250m

An Aiwatar

An aiwatar da wannan aikin na samar da magunguna da kayayyakin asibiti ga asibitoci da cibiyoyin kula da lafiya na matakin farko a ranar 15 ga Disamba 2021. Tarin kayan aikin asibiti da suka haɗa da gadaje, kujeru da katifu, kayan aikin tiyata, injin samar da wutar lantarki, da magunguna ne aka sayo aka kai wasu asibitoci a dukan ƙananan hukumomi guda hudu (4) da suka ƙunshi shiyyar ɗan majalisar dattawan.

Sai dai ba mu tantance takamaiman yawan kayayyakin da kuɗin kayan ba.







# Samar da Kayan Tallafi ga Matasa da Mata a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Arewa.

**N100m**

**An aiwatar**

Wannan aikin wanda aka ƙaddamar a ranar 17 ga Disamba 2021 yana da alaƙa kai tsaye da horon ƙarfafawa gwuiwa da aka aiwatar a cikin 2020 lokacin da aka horar da masu cin gajiyar wannan shirin a fanni daban-daban amma ba duka ne su ka sami kayan tallafi bayan an horas da su ba. Don haka, wannan shirin ya kasance na rarraba kayan ƙarfafawa ne ga waɗanda suka riga su ka amfana da horon a baya. Kayayyakin da aka sawo kuma aka rarraba sun haɗa da kwamfutocin tafi-da-gidanka, awaki (don kiwo), injin ɗinkin tela, kayan aiki (na masu fasaha), injinan yin facin taya, da kayan sana'ar kiwon kaji.

Ganin cewa an riga an rubuta waɗanda za su ci gajiyar wannan tallafi, an dauki makonni ana rabon kayayyakin. Amma ba mu da masaniya akan yawan abubuwan da aka saya da jadawalin rarraba su ba.







# Karfafawa Mata a Karamar Hukumar Kaura Namoda a Shiyyar Sanatan Arewacin Zamfara

**N14m**

**An Aiwatar**

Wannan aikin an yi shi ne musamman ga mata a ƙaramar hukumar Kaura Namoda kawai, wanda kuma mahaifar dan majalisar ke nan. Injunan ɗinkin su ne kayan da aka rarraba wa waɗanda suka ci gajiyar shirin. An zaɓo mace bakwai daga kowace cikin gundumomi goma sha ɗaya (11) na ƙaramar hukumar. Sharuɗɗan zaɓin na masu cin gajiyar, kamar yadda aka saba, ba a sani ba. Wannan yana nuna matsalar tantance sahihancin buƙatun al'umma wajen aiwatar da ayyukan tallafi a cikin Jihar.







## Tallafin Fina-Finai a Karamar Hukumar Kaura Namoda

N50m

Unknown

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

## Tallafin Fina-Finai a Karamar Hukumar Shinkafi

N50m

Unknown

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

## Tallafin Fina-Finai a Karamar Hukumar Zurmi

N50m

Unknown

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

## Tallafin Fina-Finai a Karamar Hukumar Birnin Magaji

N50m

Unknown

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.




## MAZABAR ZAMFARA TA TSAKIYA

**2** Yawan Ayyuka

**0** Aka Aiwatar

**2** Ba ayi ba

## Koyar da Makamar Sana'o'i ga Matasa da Mata a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Tsakiya.

N114m

Ba Ayi ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

## Koyar da Makamar Sana'o'i ga Matasa da Mata a Shiyyar Sanatan Zamfara ta Tsakiya

N100m

Ba Ayi Ba

Masu tantance ayyuka sun zagaya mazaɓar don tabbatar da aiwatar da wannan aikin amma duk bayani daga mutanen mazaɓar basu nuna wata alama ta an aiwatar da aikin ba.

# Tsarin Bada Matsayi

Matakin A na duban ko an yi amfani da tsare-tsaren hadin gwiwar jama'a kamar taron zauren gari don shigar da 'yan ƙasa a cikin tsarin tantancewa da zartarwa.

**Matakin A**
**40%**

Dabarun da aka yi amfani da su na ɗaukar maki ɗaya (1) rashinsa kuwa sifili (0)

Matakin B na auna aiwatar da duk ayyukan da yan majalisa suka gabatar

**Matakin B**
**35%**

Ayyukan da Aka Aiwatar / Jimillar Yawan Ayyuka

Matakin C na duba yawan ayyukan da aka gabatar tare da banbancewa tsakanin manyan ayyuka da ayyuakan horo da bada tallafi.

**Matakin C**
**25%**

Manyan Ayyukan da Aka Gabatar / Jimillar Yawan Ayyuka

# Sakamakon 'Yan Majalisa a Matakin A

Matakin A na duba ko hanyoyin haɗin gwiwar da Jama'a kamar taron zauren gari an yi amfani da su don shigar da 'yan ƙasa a cikin tsarin tantancewa da aiwatarwa.

| Dan Majalisa | Matsayi a Matakin A |
|---|---|
| SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0 |
| SEN. SAHABI YA'U | 0 |
| SEN LAWALI HASSAN | 0 |
| KABIRU AMADU | 0.4 |
| SHEHU AHMED | 0 |
| KABIRU YAHAYA | 0 |
| AHMAD MUHAMMAD | 0 |
| SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 0 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0 |
| BELLO HASSAN SHINKAFI | 0 |

# Sakamakon 'Yan Majalisa a Matakin B

Wakilan da suka yi matsayi mafi girma a kan Matakin B sun tabbatar da cikakken aiwatarwa / aiwatar da aikin da suka gabatar.

| Dan Majalisa | Matsayi a Matakin B |
|---|---|
| SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 1 |
| KABIRU AMADU | 1 |
| AHMAD MUHAMMAD | 1 |
| BELLO HASSAN | 0.75 |
| SHEHU AHMED | 0.66 |
| SEN. SAHABI YA'U | 0.66 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0.66 |
| KABIRU YAHAYA | 0.50 |
| SEN LAWALI HASSAN | 0.50 |
| SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0 |

# Sakamakon 'Yan Majalisa a Matakin C

Wakilan da ke da matsayi mafi girma akan Matakin C sun ba da fifiko akan manyan ayyuka. Waɗanda ke da ƙananan matsayi sun gabatar da ayyukan da ba a iya tantance tasirin su.

| Dan Majalisa | Matsayi a Matakin C |
|---|---|
| SEN LAWALI HASSAN | 0.50 |
| KABIRU YAHAYA | 0.50 |
| SEN. SEN. SAHABI YA'U | 0.33 |
| AHMED MUHAMMAD | 0.33 |
| KABIRU AHMADU | 0 |
| SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0 |
| SHEHU AHMED | 0 |
| SULAIMAN ABUBAKAR | 0 |
| BELLO HASSAN | 0 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0 |

# Matsayin 'Yan majalisa Na Karshe

| Matsayi | Dan Majalisa | Sakamakon Karshe |
|---|---|---|
| 1st | HON. KABIRU AMADU | 1 |
| 1st | HON. BELLO HASSAN SHINKAFI | 1 |
| 1st | HON. SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 1 |
| 1st | SEN. LAWALI HASSAN | 1 |
| 5th | SEN. SAHABI YAU | 0.99 |
| 5th | HON. AHMAD MUHAMMAD | 0.99 |
| 7th | HON. BELLO HASSAN | 0.75 |
| 8th | HON. SHEHU AHMED | 0.66 |
| 8th | HON. UMAR DAN GALADIMA | 0.66 |
| 10th | SEN.MUHAMMAD HASSAN | 0 |

## Jimillar Kudaden Ayyukkan



# N2.24BN

## YAWAN AYYUKAN DA AKA GABATAR

# 30

**4** Manyan Ayyuka

**26** Ayyukan Horo/Tallafi

ZamTracka

Data | Civic Advocacy | Social Accountability

Follow up and track implementation of public projects within your vicinity

Upload pictures, add comments, send feedback to institutions

Announce and share with your friends, family and thousand across the state

Continue to engage.

No. 40, Sadiqu Sadiq Road,
Tudun Wada, Gusau, Zamfara State.

f/t @ZamTracka

ZamTracka@gmail.com

# #AskQuestions